[HOSPITAL CONTACT DETAILS]

# GWAJIN HALT-IT
# BAYANAI GAME DA BINCIKE

**Taken bincike:** Tranexamic acid don magance matsalar zubar jini a hanji: za~I ne na kasashen duniya, tare da maganin gwaji don samun daidaituwar gwajin
**Lambar wurin gwaji**: xx
**Zubin takardar bayani:** 2.0 [Nijeriya] 23/08/2017

**Wannan asibitin tana bincike don samun maganin zubar jini a hanji**

## Aya daga cikin masu zuwa ya dace da kai:

1) Kai marar lafiya kana da zubar jini a hanji. Muna gayyatar ka shiga wannan bincike .
2) Kai marar lafiya kana da zubar jini a hanji .Idan ba ka jin dai warai an sa ka cikin wannan bincike. Muna son ka amince da shiga wannan bincike a yanzu.
3) Kai Wakilin marar lafiya ne wanda ke fama da zubar jini a hanji. Muna son ka yanke shawara a maimakon marar lafiya ko/ zai iya shiga wannan bincike. Kana iya lura ko marar lafiya ya yarda da ya shiga binciken/yana da cikakken tunanin shawara.

## Wannan aramin littafin na mene ne?

Kafin ka yanke shawarar shiga wannan bincike muna son ka san dalilin yin hakan da abun da ya kunsa. Aya daga cikin ma'aikatanmu zai tattauna da kai cikin wannan karamin littafi tare da amsa duk tambayoyin da kake da su. Muna ganin wannan zai ]auki kamar mintuna ashirin. Kana iya fa]a wa wasu game da binciken.

## Mene ne dalilin binciken?

Muna son samar da ingantaccen maganin zubar jini a hanji. Muna kyautata zaton wannan bincike na magani (kwayar da ake kira taranezamik asid), wanda zata taimaka ga daskare jini, kuma zai rage zubar jini a hanji. Amma tana iya daskare jini wajen da ba a buatar hakan.

Taranezamik asid ba sabon magani ba ne. An sha amfani da shi don dakatar da zubar jini ga mutane bayan an yi musu tiyata ko rauni a haari. Muna fatan wannan maganin zai taimaka warai ga masu fama da zubar jini a hanji duk da yake har yanzu ba mu tabbatar ba.

## Don me aka tambaye ni in shiga?

Kai (marar lafiya) kana da zubar jini a hanji kana bukatar a magance da gaggawa. Likitanka ya lura zaka iya shiga bincike, shawara ta rage gare ka ko ka shiga ko kar ka shiga.

Idan ka shiga zaka zama aya daga cikin mutane dubu goma sha biyu (12,000) masu fama da zubar jini a fa]in duniya.

## Marar lafiya ba zai shiga binciken ba idan:

- Likita ya lura akwai wani dalilin da zai hana ka amfani da taranezamik asid
- Likita ya lura akwai wani dalilin da zai sa ka yi amfani da taranezamik asid kai tasye
- Shi /it ba babba ba ne

Kai (marar lafiya) an gayyace ka ne ka shiga wannan bincike saboda babu ]aya daga cikin dalili na sama da ya dace da kai.

## Ko ya kamata in shiga?

A'a. Shawara ta rage maka ka shiga ko kar ka shiga. Idan ba ka son shiga, likitanka zai cigaba da kula da kai kuma zai ba ka duk magungunan da kake bu}ata.

## Yaya wannan bincike ke aiki?

Ba mu sani ba ko bayar da taranezamik asid da kuma sauran magunguna da aka saba zasu yi tasiri ko ba zasu yi ba. Yadda zaka gano ka dubi mutanen da suka yi amfani da shi suke, ka kwatanta su da wadanda ba su yi amfani da shi ba.domin yin haka, mutane da suka shiga cikin wannan bincike za a sa su cikin daya daga cikin sashen biyu. Sashe daya zasu nazarci maganin (taranezamik asid). [aya sashen zasu samu maganin gwaji (na rage radadi). duk sashen da aka sa mutum an za~e shi ta canki-canki kowane mutum yana da dama iri ]aya ta shiga kowane sashe. Wannan binciken magani da kuma maganin gwaji kamannin su iri ]aya ne, soboda haka kai da likitanka za ku san wane sashe kake ciki.

## Me zai faru da ni idan na shiga ciki?

Zaka samu dukan maganin da aka saba ba ka domin taimaka ma zubar jininka.kuma za a ba ka ]aya daga cikin maganin bincike (taranezamik asid ko na gwaji). Za ka fara amfani da wannan maganin nan take. Za a sa maka ta gorar ruwa har tsawon sa'o'i ashirin da hudu. Wannan magani na bincike kyauta ne. Ba ka bukatar wani gwaji ko da]ewa a asibiti soboda binciken. Zamu ba ka karamin littafi ka ajiye kuma zaka sa hannu a takardar yarjejeniya. Muna son mu aika wasi}a domin likitanka ya san kana cikin wannan binciken.

## Me zai faru bayan hakan?

Muna son mu san yanayin lafiyarka bayan ka bar asibitin. Kafin ka tafi gida za a ba ka kati ka tafi da shi. Idan ka ga likita ko nas domin wata rashin lafiya a cikin wata da zuwa asibiti, sai ka nuna musu katin.

## Me ya sa zan cutu idan na shiga ciki?

Sauran bincike ya nuna maganin bincike (taranezamik asid) ba ya haddasa daskararren jini kuma babu wani mummunan sakamako domin yin amfani shi na wani lokaci, amma fa ba a san ko wannan zai yi daidai ga mutane masu irin yanayinka ba. Likitanka zai kula da kai kuma zai ba ka kulawa mafi kyau idan akwai wata matsala. Kuma zasu sanar da mutanen da ke gudanar da shirin.

## Ko zan amfana idan na shiga ciki?

Ba mu sani ba ko wannan bincike zai taimaka maka. Amma zai taimaka wa likita sanin yadda zai ba da maganin zubar jini a hanji nan gaba.

## Ko zan iya sauya ra'ayina game da shiga ciki?

E. Idan ka sauya ra'ayinka game da shiga ciki, kawai sai ka sanar da likitanka cewa ba ka son ka cigaba da binciken. Kana iya yin haka a kowane lokaci. Likitanka zai kula da kai kuma zai ba ka sauran kulawa. Maganin da kake bukata. Muna fatan zaka ba mu damar

samun bayanin game da yadda ka kamu, amma idan ba ka son mu yi amfani da shi sai ka fada ma likitanka.

## Wane irin bayani ake nema a gare ni?

Bayanai game da zubar jininka, maganin da ka samu kuma ta yaya ka same shi duk za a rubutu. Ma'aikatan da ke babban ofishin Landan zasu karbi kwafin takardar yarjejeniya da ka sa wa hannu.

## Ko za a asirta bayanaina?

Dukkan bayanai da aka karba game da kai za a ~oye su. Mutanen da za a ba damar duba bayani su ne likitocin da ke gudanar da binciken, ma'aikatn babban ofishi a Landan da kuma masana masu duba ingancin bincike da kyau.

Likitanka zai aika wasu bayanai game da kai ga kungiyar bincike a Landan domin su adana da kyau. Za a adana bayananka na sirri daban tare da sauran bayanan bincike kuma za a kone bayanan bayan shekara biyar da gama bincike.

Za a buga sakamakon bincike a jaridar kungiyar likitoci domin kowane likita ya gani kuma ya koya daga gare su. Amma ba za a buga bayananka na sirri ba a cikin bayanin binciken kuma babu yadda za a gane daga wannan.

Bayanan binciken za ya]a su a duniya domin a yi amfani da su don inganta ilimin ~angaren lafiya da marasa lafiya a duniya don masu nazari da bincike. Amma ba za a buga bayananka na sirri ba a cikin bayanin binciken kuma babu yadda za a gane daga wannan.

## Wa zai biya domin wannan bincike?

Gwamnatin kasar Burtaniya ce zata biya. Ba za a biya likitanka ba don ya sa marar lafiya cikin wannan bincike. Za a samar da ku]in da ya shafi wannan gwajin ne kawai.

## Wa ya duba wannan bincike?

Don kare ra'ayinka, dukkan bayanai na bincike da aka samu a wannan asibiti sai wata kungiya mai zaman kanta ta duba da kyau wadanda ake kira da kwamitin kula da halayyar bincike. Wannan bincike an duba shi a tsanake kuma an ba da shaidar ingancinsa daga (Insert name) Research Ethics Committee da kwamitin kula da halayyar bincike. Idan kana da wata tambaya da ta shafi 'yancinka, ko kuma kana ganin an tauye maka hakki a matsayinka na mai halarta, zaka iya tuntu~ar shugaba ta wannan adireshi na kasa:

| | |
|---|---|
| Sunan shugaba | |
| Adireshi | |

An aminta da bincike a Najeriya:
Daraktan. Rajistar harakokin waje
Hukumar kula da yaki da masu safarar miyagun kwayoyi (NAFDAC) 445, Herbert Macaulay Way, Yaba, Lagos, Najeriya
Lamb.waya: 01 477 2452

## Ko zan iya samun sakamkon binciken?

Wannan bincike zai are shekara ta dubu biyu da ashirin 2020. Idan kana son ta}aitaccen bayanin sakamakon wannan bincike da aka gama yanzu, ka sanar da likitanka da ke kula da kai. Zaka iya ziyarar shafin binciki domin ka ga cigaba (haltit.Lshtm.ac.uk).

## Wa zan tuntuba idan ina da tambaya ko wata damuwa?

Idan kana da tambaya ko damuwa game da wannan bincike, an ba ka damar ka tattauna tare da likitocin bincike zasu yi matukar }o}arin su amsa tambayoyinka . Lik. (PI name) mai kula da wannan bincike a wannan asibitinl. Zaka iya tuntu~ar likitan ta:

| | |
|---|---|
| Adireshi | |
| Lamb.waya | |

Kuma Zaka iya tuntu~ar babban Daraktan Kiyon Lafiya na asibitin:

| | |
|---|---|
| Sunan Daraktan | |
| Adireshi | |
| Lamb.waya | |

Idan ba ka gamsu ba kana son ka kai kokenka a }a'idance, kana da dama ta hanyoyin gabatar da koke-koke na asibitin. Ka tabbata ka tambayi masu bincike don Karin bayani. Likitoci da kungiyar masu gwaji suka tsara wannan bincike a kwalejin kimiyar tsabta da magungun ta Landan (jami'ar Lanndan). Za a iya tuntubar su:

| | |
|---|---|
| Adireshi | HALT-IT Trial Coordinating Centre, London School of Hygiene & Tropical Medicine, Room 180, Keppel Street, London WC1E 7HT, United Kingdom |
| Lamb.waya | +44 (0)20 7299 4684 |

## Me kuma ya kamata in sani?

Idan an samu wata matsala har ka ji ciwo a wannan bincike, saboda sakacin wani, kana da damar neman a biya ka diyya. kwalejin kimiyar tsabta da magungun ta Landan, wadanda suka shirya shirin, zasu dauki alhakin biyan duk wanda ya samu wata matsala saboda sakaci sakamakon shiga wannan bincike.

Ana karfafa maka ka tambayi wanda ka ga dama, kafin, yayin ko bayan an kare binicke. Idan kana da wata tambaya game da bincike, ka tattauna da likitanka ko nas, wanda zai iya ba ka bayanan da ake ciki game magunguna/hanyoyin amfani da su. Idan kana son karanta bincike game da wannan bincike, sai ka tambayi likitanka ko nass.